**KOMAI NISAN JIFA**

**EPISODE 7**

Characters

*Asabe*

*Jummai*

*Danjuma*

*Tina*

*Husseini*

*Eze*

*Hannah*

---

**Episode 7, Scene 1**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's Residence. Morning.**

1. **MUSIC:** **THEME MUSIC**

2. **SFX:** **SOUND OF CHICKS IN THE COMPOUND. FOOTSTEPS AS JUMMAI MAKES TO LEAVE THE HOUSE. FOOTSTEPS OF ASABE MOVING CLOSER.**

3. **ASABE:** **(CALLING OUT, OFF-MIC)** Jummai! Jummai!!! Jummai dakata!

4. **JUMMAI:** **(ON-MIC, SURPRISED)** Naám? Asabe? Lafiya?

5. **ASABE:** **(COMING ON-MIC, BREATHLESS)** Jummai, yaki, ban gane miki a gidan nan ba fa.

6. **JUMMAI:** **(SURPRISED)** Ne? Me na ye?

7. **ASABE:** Jummai, dubi yadda kike tafiya zuwa wurin aiki kamar komai lafiya lau, bayan kin san akwai tashin hankali.

| | | |
|---|---|---|
| 8. | **JUMMAI:** | **(CONFUSED)** Tashin hankali, a ina? Asabe, menene kike cewa, ki hanzarta kada in makara. |
| **9.** | **ASABE:** | **(CLAPS HANDS TOGETHER)** Oh ho, ke kada ki makara zuwa wajen aiki ne damuwar ki, bayan yar shishigin nan Laraba tana son kwace mana gida. |
| 10. | **JUMMAI:** | Asabe, bana fahimtar abinda kike fada, yaya Laraba yaza ta kwace mana gida bayan ita yar hay ace, kuma shiru shiru. |
| ~~11.~~ | **ASABE:** | **(ANGRILY)** Wato baki lura da yadda take kusantar Inna a cikin yan kwanakin nan bane? Har ma akai tana iya hana Inna cin wasu girkin mu. |
| **12.** | **JUMMAI:** | Amma Inna tace wai sabada da lafiyar ta ne ai. Menene lafin hakan? |
| **13.** | **ASABE:** | Wace irin zancen banza ne haka! Bata minti biyar ba har ta fara zargin muna takura ma Inna, muna bata abincin da bai dace da lafiyar taba. |
| 14. | **JUMMAI:** | Amma ta yaya ki ka san dukan wadan nan abubuwan? ni ban yarda ba. |
| **15.** | **ASABE:** | **(UPSET)** Jummai, kina nufin ni makaryaciya ce kenan? |
| **16.** | **JUMMAI:** | Samsam, amma Inna ta fada min cewa tana son ta rage cin nama da gishiri saboda Laraba ta damu da yadda jinin ta ked an hawa. |
| **17.** | **ASABE:** | **(ANGRILY)** Hakika! Tana kokari Inna taso ta ne ai |
| **18.** | **JUMMAI:** | Amma Asabe, har wanda suka dauki ni aiki ina nufin su Jiyas sun dau irin wannan matakin dagane da abincin da suke ci, kin san Inna ta tsufa ai. |
| 19. | **ASABE:** | **(DISAPPOINTED)** Haba Jummai! Me ke damun ki ne? A wurin ki ina surutu kamar mahaukaciya ko, abinda nake fada wautanci ne ko? |

20. **JUMMAI:** Ni ba abinda nace ba kenan, kina dai tada hankalin ki akan abinda bai kai ba ne dai, Kuma kin san dole in tafi aiki, sai na dawo.

**21. ASABE:** **(DISAPPOINTED, ANGRILY)** Ehhnn Jummai! Na ga kema kina goyon bayan Laraba, toh kin san cewa baza a gama lafiya ba!

**22. MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 7, Scene 2**

**Southern Kaduna. Danjuma's Office. Afternoon.**

**23. SFX:** **SOUND OF KNOCK ON DOOR**

**24. DANJUMA:** **(ON MIC, CALLING OUT)** Shigo.

**25. SFX:** **SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING**

**26. TINA:** **(COMING ON MIC)** Ina yini yaya Danjuma

**27. DANJUMA:** Ahhh Tina, kice? Yaya aiki yau kuma?

**28. TINA:** Erm Yaya Danjuma Lafiya Lau, na kawo wannan fayil din domin ka sa hanu, na sake dubuwa sosai kamar yadda ka fada min.

**29. DANJUMA:** Yayi Kyau Tina, ki ajiye anan, idan na shirya zan kirawo ki.

**30. TINA:** Toh Yallabai. Akwai abinda kake bukata ne?

**31. DANJUMA:** **(DISTRACTED)** Aá nagode. **(SUDDENLY AWARE)** Yauwa, ina fatan kina jin dadin batar kasan naki anan

**32. TINA:** Tabas, sai dai inna famar in gani wasu abubuwa har yanzu, amma da dadi.

33. **DANJUMA:** Yayi kyau. Nasan zaki fuskanci abubuwa sosai masaman ma idan zaki yi biyyaya da wadan da suke nan kafin ki zo da kuma abukan aikin ki.

**34. TINA:** Naám, yaya Danjuma

35. **DANJUMA:** Kuma kada kiyi girman kai wajen tabayar abin day a shige miki duhu.

36. **TINA:** Naám yallabai. Zan yi kokarin koyan duk abinda yakamata kafin lokucin bautar yak are.

**37. DANJUMA:** Yayi kyau, toh zan kira ki idan……

**38. TINA:** **(CUTS IN)** Her, Yaya Danjuma, ina son in yi amfani da wannan dammar in gode maka mutuka daka bani masauki da dammar yi bautar a nan.

**39. DANJUMA:** Toh, amma ki gode wwa yarúwar ki, Hannah da ta amince miki ki zauna a gidan, saboda itace ki son kid a zama a gidan.

**40. TINA:** Ita ai ya zaman mata kamar dole ne ai, tunda muna da dangi. Amma kai yaya Danjuma ai bai zama maka dole ba ai.

41. **DANJUMA:** **(EMBARRASSED)** Toh ba matsalla. Yanzu zan maida yanúwan Hannah tamkar yanúwa na ai. Ga wannan fayel din ki kai ma mallam Ibro.

**42. SFX:** **<u>SOUND OF FILE AND SOME PAPERS RUSTTLING.</u>**

**43. TINA:** Toh Yallabai

**44. SFX:** **<u>SOUND OF HIGH HEELED FOOTSTEPS WALKING AWAY</u>**

**45. DANJUMA:** **(CALLING OUT)** Tina! Dakata. Ya ki.

**46. SFX:** **<u>SOUND OF COUNTING MONEY</u>**

**47. TINA:** **(CONFUSED)** Naám yaya Danjuma?

48. **DANJUMA:** Ga wannan ki kara ma kudi abincin ranan ki, na san abin da ake baku ba yawa.

49. **TINA:** **(VERY HAPPY)** Yaya Danjuma, Nagode! Ba zaka san abinda wannan zai yi min ba.

50. **DANJUMA:** **(EMBARRASSED)** Toh, ki hanzarta ki kai ma Mallam Ibro fayel din.

**51.** **TINA:** Ah! Nagode sosai yallabai. Kana kyauta min kwarai.

**52.** **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 7, Scene 3**

**Northern Kaduna, Hussaini's Mai Shayi Spot. Afternoon**

**53.** **SFX:** **SOUND ROAD AMBIENCE WITH DISTANT SOUND OF MOVING CARS AT RANDOM.**

54. **HUSSAINI:** Ahh! Eze wato kaima kaje labarin sabuwar rumfa ta kenan?

55. **EZE:** **(EXCITEDLY)** E wallahi Husseini. Shine ma dalilin da na zo, **(LAUGHS)**

56. **HUSSAINI:** Ah Eze ka zauna, bara in kawo abin sha

57. **SFX**: **SOUND OF A BENCH SCRAPING THE GROUND AS EZE SITS**

58. **EZE:** Kamar kasuwar tana kaima maka fa, kana da abokan ciniki da dama, wajen ma ya dace da sanaár

**59.** **HUSSAINI:** E sai godiyar Allah, fata na in sami ciniki sosai saboda in iya kula da iyali na wato matata da yayana.

60. **EZE:** Haba Husseine, kafiye damuwa fa! Kasuwar zata kankama sosai ai kuma komai zaiyi kyau.

**61.** **HUSSAINI:** Ni ma na san dahaka, a gode da karfin guiwan da kake bani Eze.

**62. EZE:** Ba damuwa ai kai nawa ne. **(TEASING**) masamman ma in zaka dinga kawon min lemu karma haka duk lokacin da abin alheri ta same ka.

**63. HUSSAINI:** Kai dai Eze! Kafiyen son baza sosai. Ka ma tuna min, kun taba haduwa da sabuwar Nars din da aka kawo nan alúmar kuma.

64. **EZE:** E mun hadu fa. Tazo ta gayace ni in shiga kungiyar inganta lafiya anan alúmar data ke son ta fara

65. **HUSSAINI:** **(TEASING)** Wow Eze. Wannan ya nuna cewa kai babbar mutum ne.

**66. EZE:** **(LAUGHING)** Ah Husseini, ai ba karamin abu bane?

67. **HUSSAINI:** Kasan a cikin gidan mu take da zama ai.

68. **EZE:** Ah yayi kyau. Ya dace da ta samu gida mai mutunci a alúmar kamar gidan babar ka. Hankalin ta zai fi kwanciya.

**69. HUSSAINI:** Tama taimaka wajen sake ma Inna abincin da yakamata ta dinga ci saboda samun koshin lafiyarta.

70. **EZE:** Eyyah! Toh Husseine ya Hajiya Inna take?

71. **HUSSAINI:** Ta ji sauki sosai, kuma saukin ma na saki karuwa

**72. EZE:** Zan same lokaci in zo in duba ta, ka dai gaida min da ita fa

73. **HUSSAINI:** Ba matsala **(PAUSES)** Eze, ko ka san duk lokacin da na dubi rumfar nan sai inji wani irin dadi ya cika ni

74. **EZE:** E mana, abu mai kyau ne ai ta same ka, dole ni ka dinga jin dadi ai.

**75. HUSSAINI:** Hmm Eze, ina mutukar godiya ma Alhaji Bature, ya tallafa min sosai ya taimaka kwarai

**76. MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Episode 7, Scene 4**

**Southern Kaduna. Danjuma and Hannah's Residence. Evening.**

| | | |
|---|---|---|
| **77.** | **SFX:** | **SOUND OF PLATES BEING STACKED FOR CLEARING** |
| **78.** | **DANJUMA:** | **(ON MIC, CALLS OUT)** Hannah, taho mu zauna, zan taimaka miki daukan kwanuka zuwa kicin anjuma |
| **79.** | **HANNAH:** | **(TEASING, COMING ON-MIC)** Ka tabbata Danjuma? Ko dai anjuma zakana cewa a gajiye kake? |
| **80.** | **SFX:** | **SOUND OF FURNITURE CREAKING AS HANNAH SITS** |
| **81.** | **DANJUMA:** | Haba Hannah! Kina nufin ban taba taimaka miki a kicin ba? |
| **82.** | **HANNAH:** | **(LAUGHING)** Zacen gaskiya, kana yi. Ka iya wanke wanke kwanuka sosai ma. |
| **83.** | **BOTH:** | **(LAUGH)** |
| **84.** | **DANJUMA:** | **(TEASING)** Ehn amma yanzu da yarúwan ki take nan bana samun in taya ki, ina kewar wankewanke ma |
| **85.** | **HANNAH:** | **(LAUGHING)** Amma kasan cewa za ka iya zuwa ka taimaka ko da yaushe ai, amma kayi gaskiya fa Tina na mutukar taimako na fa. |
| 86. | **DANJUMA:** | Tina tana taimakawa sosai a ofis fa, tana da kwazo da ladabi. |
| **87.** | **HANNAH:** | Na yi murna **(CLEARING THROAT, GIGGLING)** |
| **88.** | **DANJUMA:** | Ahn Ahn Hannah! Me kike tunani da kike gyara murya. |
| 89. | **HANNAH:** | **(STILL GIGGLING)** Toh Danjuma. Ina ganin zacen dadi ne yasa naki gyarar murya. |
| **90.** | **DANJUMA:** | Haba? Toh ina ji ki. |
| **91.** | **HANNAH:** | **(SHYLY)** Danjuma, inna da juna biyu! |

| | | |
|---|---|---|
| **92.** | **DANJUMA:** | **(SURPRISED)** Me!? Kin tabbata? Da gaski kike? |
| 93. | **HANNAH:** | Na je naga Laraba saboda ina jin laulayi, bayan nayi mata bayani, sai ta auna ni. |
| 94. | **DANJUMA:** | **(EXCITED)** Abi Mamaki! Na yi murnan ji wannan zancen, ban san ba wuyar samun juna biyu bayan amfani da kwayoyin tazarrar haihuwa. |
| **95.** | **HANNAH:** | Ni ma haka, masoyi na **(EMOTIONAL)** Danjuma ciki nakeda da murna. |
| 96. | **DANJUMA:** | Ina son ki fara rubuta abinda kike bukata ma kanki dana jaririn |
| **97.** | **HANNAH:** | **(LAUGHING)** Aháh! Tun yanzu? Muna da lokaci dayawa fa. Bana zaton muna bukatar abu na musamma yanzu . |
| **98.** | **DANJUMA:** | Ya masoyita, kin san bai yi wuri ba fa idan mun fara nazarin muhimman abubuwa kamar makarantar da yaran mu za su je da kuma yadda zamu biya. |
| **99.** | **HANNAH:** | **(HAPPY)** ina son yadda kake tunani ka Danjuma, Danjuma kai maji na gari ne kuma haka ma za ka za uba na gari. |
| **100.** | **DANJUMA:** | **(HAPPILY)** Ah amma tare da mace mai fahimta kamar ki abubuwa sun yi sauki ai. Hannah bana tunanin akwai abin da zai kawo mana matsalla a yadda muke da gida ciki da zaman lafiya. |
| **101.** | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |